# Misalin wanda yake ambatan Ubangijinsa da wanda ba ya ambatan Ubangijinsa, kamar rayayye ne da matacce

Daga Abu Musa - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi - ya ce: "Misalin wanda yake ambatan Ubangijinsa da wanda ba ya ambatan Ubangijinsa, kamar rayayye ne da matacce", lafazin Muslim kuma: "Misalin gidan da ake ambatan Allah a cikinsa, da gidan da ba'a ambatan Allah a cikinsa, kamar rayayye ne da matacce".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bayyana banbanci tsakanin wanda yake ambatan Allah - Maɗaukakin sarki - da wanda ba ya ambatanSa, kuma misalin banbanci ne tsakanin rayayye da matacce a anfaninsa da kyakkyawan zahirinsa, misalin wanda yake ambatan Ubangijinsa misalin rayayye ne wanda a zahirinsa mai adone da hasken rayuwa, kuma baɗininsa da hasken ma'arifa, kuma a cikinsa akwai anfani, kuma misalin wanda ba ya ambatan Allah kwatankwacin mamaci ne wanda zahirinsa ba ya anfani, kuma baɗininsa ɓataccene, babu wani anfani acikinsa. Haka nan gidan da ake siffanta shi da rayayye idan mazaunansa sun kasance suna ambatan Allah, inba haka ba to shi mataccen gida ne, saboda barin mazaunansa daga ambatan Allah; idan an wawaita mamaci da matacce a cikin siffanta gida kawai ana nufi da shi mazaunin gidan.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee